# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Aljannar Kare – Haɗarin afkawa cikin bashi
## Kashi na takwas: Sakamako

Wanda ya rubuta: James Muhando
Wanda ya fassara: Danlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

Mai ba da labari: ɗan shekara 30
Lawan: ɗan shekara 40
Nana: 'yar shekara 35
Malam Audu Sani: ɗan shekara 40
Shaƙiyyiyar ɗaliba: 'yar shekara 15
A'i: 'yar shekara 15
Mai gidan wankin mota: ɗan shekara 30
Bash: ɗan shekara 15
Ali: ɗan shekara 15
Jamila: 'yar shekara 15
Ligidi: ɗan shekara 17

**Mai ba da labari:**

Masu sararenmu, barkanmu da sake saduwa a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu". Wannan shi ne kashi na takwas na wasan kwaikwayon nan namu mai taken "Aljannar kare – Haɗarin afkawa cikin bashi". Ina kuma yi muku maraba da saduwa a cikin wannan ɗan ƙaramin ofis ɗin nawa da nake aiki a cikin banki a matsayin mai ba da basussuka. Idan ba ku manta ba dai sunana Aliyu Bello, ko kuma Ali, kamar yadda ake kirana. Kuma ni ne jagoran wannan shiri.

To kamar yadda aka saba, zan ci gaba da ba ku labarin yadda rayuwar nan tawa ta ƙuruciya ta kasance. Idan kuna biye da ni, kun ji yadda aka kama azzulumin mai bayar da bashin nan, wato Malam Ado, saboda laifin karya hannun Jamila a lokacin da yake ƙoƙarin karɓar kuɗinsa da ya ara mana. Haka kuma kun ji yadda aka yanke wa Kawu Natanko hukunci a kotu saboda ya kasa biyan basussukan da ake binsa. To, haka kuma shi ma abokina Bash ya samu kansa a cikin matsala bayan da ya sayi keke bashi kuma ya kasa biya. Hakan ta faru ne kuwa bayan da babansa ya dawo daga tafiya, ya ji labarin abin da ɗansa ya aikata.

**Fitowa ta 1: A gidan su Bash**

| | |
|---|---|
| **Lawan:** | Nana! Nana! Buɗe wa mijinki ƙofa mana, ga ni na dawo gida da borin kunyata! |
| **Nana:** | Kai wannan babanka ne kuwa? Na ji kamar a buge yake. Kuma na san babanka ba ya shan giya! |
| **Bash:** | Amma gaskiya Mama, ba na jin a buge yake! |
| **Nana:** | To, je ka ka buɗe masa ƙofa mana! |
| **Lawan:** | Wa nake gani haka? Me wannan shaƙiyyin yaron yake yi a gidana? Ban gaya miki cewa ba na so in ƙara ganinsa a gidana ba? |

**Nana:** Haka ne, Maigida? Ko a buge kake ne?

**Lawan:** Yaya za ki amsa mini tambaya da tambayar! Ki ba ni amsar tambayar da na yi miki kawai!

**Nana:** Tsaya ka ji Maigida, wannan fa ɗanka ne. Ya riga ya yi kuskure kuma an ladabtar da shi!

**Lawan:** Kuskure? Yaron da ya sa na ji kunya a gaban abokaina da kuma mutanen wannan ƙauyen! Yanzu ga shi maƙiyana sai murna suke ta yi abin kunya ya same ni! Kuma wai har shi ne za ki kira shi kuskure?

**Nana:** Maigida, don Allah ka daina dagula abin. Na roƙe ka. Za mu samu mu biya kuɗin rediyon da Bash da abokansa suka ɗauka.

**Lawan:** Idan kin yarda cewa akwai shugaba a gidan nan, to ki zaɓi ɗaya: ko dai ya bar gidan nan ko kuma ni in bari!

**Nana:** Don Allah Maigida, ka bar wannan magana mana! Don Allah!

**Bash:** Shi ke nan Mama, ki bari kawai! Ni bari na tafi.

**Nana:** Ina za ka je? Na ce ina za ka?

**Bash:** To Mama, ina da gidan abokai ai, kuma zan iya zuwa in je in zauna a wurin kakata.

**Nana:** Ba inda za ka, ka ji! Ina da kuɗin da na tara, bari na ba ka su ka je ka biya kuɗin rediyon gobe da sassafe kafin ya

tashi daga barci.

**Bash:** To Mama, na gode!

**Mai ba da labari:**

To ni dai kam yanzu da nake aiki a banki da kuma da lokacin da nake bagidajena, babu wani bambanci. Kuma ko ba komai, wannan jami'in 'yan sanda ya nuna mana shi mai dabara ne, kuma ya yi mana horo ta hanyar ilimantar da mu saboda sakarcin da muka yi. Domin kuwa ya gayyaci wani ƙwararre a kan harkokin ba da basussuka don ya zo ya yi mana lacca a kan yadda ake karɓa bashi da kuma biya.

**Fitowa ta 2: A makaranta**

**Malam Audu:** Yara, kun tashi lafiya? Sunana Audu. Ina aiki ne a 'Jubilee Bank' a matsayin mataimakin manaja. Wannan jami'in 'yan sanda ne, da kuma malamarku Malama Rabi, wadda matata ce, su suka neme ni da na zo na yi muku bayani a kan matsalar karɓar bashi. To, kafin na fara zan so na ji me kuka fahimtar da kalmar bashi? Akwai wanda ya sani? Ke da kika ɗaga hannu, me ake nufi?

**Shaƙiyyiyar ɗaliba:** Bashi dai na nufin Bash!

**Malam Audu:** Abin ban dariya! To akwai wani kuma wanda zai mai da hankali ya ba mu amsa? Yauwa, ga wata can. Yaya sunanki?

**A'i:** Sunana A'i.

**Malam Audu:** Yauwa, A'i. Me ake nufi da kalmar 'bashi'?

**A'i:** Kalmar bashi na nufin yin rance.

**Malam Audu:** Da kyau! Bashi dai na nufin a ba mutum aron kuɗi na ɗan wani lokaci. To me ya sa mutane suke cin bashi? Amsar da za mu bayar a nan ita ce, mutane sukan ci bashi ne domin suna da waɗansu buƙatu na gaggawa da dole ne su warware su nan take!

**Shaƙiyyiyar ɗaliba:** Kwarai kuwa! Kamar dai sayen keke!

**Malam Audu:** Idan har mutum ya karɓi bashi, kuma ya kasa biya a kan lokacin da aka ajiye mukan ce ya yi 'taurin bashi'.

**Mai ba da labari:**
Akwai dai ilmantarwa a cikin tattaunawar da aka yi. Sai dai kuma gani nake yi a banza domin kuwa wanda ya kamata a ce ya amfana, wato Bash, ba ya ma cikin ajin a wannan rana! To shi kuwa ina ya tafi? Bayan da babarsa ta ba shi Dala 60 don ya je ya biya kuɗin rediyon Kawu Natanko da muka ɗauka a gidanmu, ashe bai je ya biya babata kuɗin ba! Yau sati guda ke nan babu wanda ya sa Bash a ido. Yanzu ga wani hargitsin can ya taso a cikin gidansu!

**Fitowa ta 3: A gidan su Bash**

**Lawan:** Ki je ki fito mini da ɗana yanzu-yanzu! Wai ina ma kika ɓoye mini shi ne?

**Nana:** Don Allah tsaya, Maigida! Wai ban gane ba, laifina kake gani yanzu, ko me?

**Lawan:** Ni dai so nake na ga ɗana kawai!

**Nana:** *"Ki gaya masa ba na son na ƙara ganinsa a nan gidan!"* Wai ba kai ka faɗi haka ba? Yanzu kuma sai ka zo ka ga laifina?!

**Lawan:** Ke fa kin ɗauka ban san cewa kin ba shi kuɗi kin ce ya je ya ɓuya ba ko?

**Nana:** Kai kuwa yaya ma za ka zarge ni da cewa na ɓoye shi, bayan da ni da kai muka duba ko'ina ba mu gan shi ba? Ya kamata Maigida, ka dinga faɗin abin da ya kamata!

**Lawan:** Yanzu ni kike cewa ban san abin da ya kamata ba? Ke fa kin ɗauka da wasa nake ko? To, ki fita ki bar mini gidana! Ba na son in ƙara ganinki a gidan in dai ba tare da Bash za ki dawo ba!

**Nana:** To ni kuwa yanzu a ina zan gan shi?

**Lawan:** A inda kika ɓoye shi za ki gan shi!

**Nana:** Tsaya Maigida!

**Lawan:** Ki fice! Fice mini daga gida na ce!

**Nana:** To shi ke nan, ba koma! Kar kuwa ka kuskura ka zo bikona!

**Mai ba da labari:**

Yanzu dai abokina ya gudu zuwa wani gari da ke kusa da mu bayan da ya samu kuɗi daga wajen babarsa. Ai bai ɗauki fiye da sati biyu ba ya kashe kuɗin da babarsa ta sha wahala ta tara, domin kuwa a hotel ya sauka kuma a can yake cin abinci. Aikin da ya samu kawai shi ne na wankin mota inda ba a

biyansa komai sai dai a ba shi abincin rana.

**Fitowa ta 4: A gari kusa da Kwazaye**

**Mai gidan wankin mota:** Kai, ɗan kauye! Ka kuwa wanke motocin nan kamar yadda na ce ka yi?

**Bash:** E, na wanke su.

**Mai gidan wankin mota:** Maƙaryacin banza! Wane ne zai kalli waɗannan motocin ya ce ka wanke su kamar yadda aka ce ka yi? Kalli wilinsu, duk ga tabo nan a jiki!

**Bash:** Wallahi Yallaɓai, sau uku ina wanke su fa, kuma akwai sauran motoci guda goma da zan wanke, kuma ga shi dare ya riga ya yi. Yaushe har zan samu na gama?

**Mai gidan wankin mota:** Kai fa ɗan kauye ne malalaci! Kama gabanka, kuma yau ba abin da za a biya ka!

**Bash:** Gaskiya ne! Sai ka ce da ma biyana yake yi!

**Mai gidan wankin mota:** Sake faɗa na ji! Me kake cewa?

**Bash:** Ba komai, cewa na yi ka yi haƙuri Yallaɓai. Don Allah kada ka kore ni, zan yi iya ƙoƙarina!

**Mai gidan wankin mota:** Ku fa mutanen ƙauye kuna da mantuwa. Ba kwanan nan ka zo min cikin tsumma da yunwa ba? Yanzu ga shi ina ba ka abinci amma kana neman ka kangare mu ko?

**Bash:** Ka yi haƙuri.

**Mai gidan wankin mota:** To na ji, ka koma bakin aikinka! Sai dai kuma yau abincin rana rabi zan ba ka!

**Bash:** To, ba komai Yallaɓai, na gode.

**Mai ba da labari:**
Idan Bash ya tashi daga aiki a lokacin da kowa yake tafiya gida ya kwanta, shi sai ya yi kamar za shi gida, amma sai ya yi kwanto ya shiga cikin rumfar wankin motoci ya kwanta tun da dai ba shi da inda za shi ya kwana. Domin kuwa shi a ganinsa, yanzu ba shi da wasu masu ƙaunarsa a gida. Sai dai kuma abin da bai sani ba shi ne, mu duk mun damu da halin da yake ciki! Kuma mun ci gaba da nemansa. To, bayan waɗansu watanni, a lokacin da ni da Jamila muka gama jarrabawa ke nan, sai…

**Fitowa ta 5: A hanya**

**Ali:** Yaya jarrabawar lissafin ta yau?

**Jamila:** Gaskiya ta yi wahala! Amma in Allah Ya yarda zan haye. Kai fa?

**Ali:** Na ji daɗinta, musamman ma dai tambayar nan ta nemo riba a kan uwar kuɗi!

**Jamila:** Ai da ma dai kai gwanin lissafi ne. Wai har yanzu kana son ka yi karatun lauya ɗin kuwa a jami'a?

**Ali:** Ina! Yanzu na bar wannan zancen. Ni yanzu so nake kawai na yi aikin banki. Saboda haka ma zan je ne na yi karatun harkokin kuɗi. …

**Ligidi:** Kai fa ka ɗauka ba zan taɓa kama ka ba ko? Zo ka ba ni kuɗina!

**Bash:** Kuɗin me?

**Ligidi:** Kuɗin da ka ranta a wurina kafin ka tsere!

**Bash:** Ai so nake na biya kuɗin keken da ka lalata mini!

**Ligidi:** To, zan nuna maka cewa kowa yana tsoron Ligidi.

**Bash:** To, ni yanzu ba tsoronka nake ji ba! …

**Jamila:** Kai! Ai wancan kamar Bash?

**Ali:** Shi ne. Me ya faru? Duk ya fita daga hayyacinsa!

**Jamila:** Ga shi can suna faɗa da Ligidi! Mu yi sauri mu raba su!

**Jamila/Ali:** Kai! Ku tsaya haka! Bash! Magana ake yi muku! Kai Ligidi! Ku bari!

**Mai ba da labari:**
To bayan 'yar wannan ziyarar da Bash ya kawo sai da aka shafe shekaru biyu kafin ya sake dawowa. A lokacin kuwa tuni ya fara shan giya da taba. Duk yunwa ta kama shi, ga kuma ƙazanta. Kuma da ya zo sai ya sake shiga cikin wani rikicin. Na san wasu daga cikinku halinsu iri ɗaya ne da na Bash, kukan yi ƙoƙarin ranto kuɗi domin sayen kyamarori ko kuma wayoyi da ake yayi. Amma kuma ba kwa ganin cewa wannan labari na Bash ya ishe mu misali? To, ni kam a ganina ya isa! Wannan ne ma dalilin da ya sa na fara aikin banki kuma nake ba wa matasa shawara a kan cin bashi.

To masu saurare, yanzu dai ina da mitin. Amma idan mun sake saduwa zan gaya muku yadda Bash ya dawo cikin hankalinsa ya kuma ladabtu. Kafin wannan lokacin za ku iya bin shirinmu na "Ji Ka Karu" a shafinmu na yanar gizo a dw.de/lbe, ko kuma ku tuntuɓe mu a shafinmu na 'Facebook'. Mun gode, ku huta lafiya!